# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Allah ya daukaka Yusuf Bawan




**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: M. Maillot; Lazarus Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Sarah S.**



**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**

**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**




**An sa Yusuf a kurkuku ba da laifi ba daga maigidansa na da, Fotifa. A cikin kurkukun, Yusuf ya kasance cikin biyayya da taimako. Mai lura da kurkukun ya amince da Yusuf domin ya gudanar da rayuwar 'yan kurkukun. Saboda Allah yana tare da Yusuf, kurkukun ya zama wurin mai kyau a wurin kowa da kowa.**




Mai yi wa sarki gurasa da mai lura da abincin sarki su ma suna a kurkukun. “Me yasa kuke cike da bakin ciki?” Yusuf ya tambaye su wata rana.
3


“Babu wani wanda zai fasara mana ma’anar mafarkunmu,” masu cike da bakin ciki suka amsa. “Allah zai iya!” Yusuf ya ce. “Ku fada mini mafarkun.”
4


“Mafarkinka yana nufi cewa kwanaki uku daga yanzu za ka sami alheri daga Sarki Firauna,” Yusuf ya gaya wa mai yi wa sarki gurasa. “Ka tuna da ni kuma ka roki Firauna ya ba ni ‘yanci.” Mafarkin mai lura da abincin sarki ba mai dadin ji ba ne. “Kwanaki uku daga yanzu za ka mutu,” Yusufya ce. Mafarkai biyun nan suka zama gaskiya.
5


Amma mai lura da abincin sarki ya manta da Yusuf har sai da Firauna ya tashi da damuwa wata rana. “Na yi wani mafarki,” ya yi kuka. Babu ko daya daga maza masu hikima na Firauna wanda ya iya nuna ma’anar mafarkinsa. Sai mai lura da abincin sarki ya tuna da Yusuf a kurkuku. Sai ya fada wa Firauna game da shi.
6


Firauna ya aika a kirawo Yusuf nan take. “Mafarkinka sako ne daga wurin Allah,” Yusuf ya gaya wa sarki. “Masar zai kasance da yawan abinci na shekaru bakwai, sa’an nan shekaru bakwai na tsananin yunwa.”
7


“Ka Shirya yanzu yadda za ka yi ajiyar abinci na shekaru bakwai;” Yusuf ya ba wa Firauna shawara, “ko kuma yunwa ya kashe mutanenka a lokacin yunwan.” “Allah yana tare da kai,” Firauna ya ambata. “Za ka lura da Masar, a matsayi mai biye da ni.”
8


Shekaru bakwai na yalwata suka zo. Sa'annan shekaru bakwai na yunwa. Ko'ina an yi rashin abinci sai dai Masar inda suka yi wayo na ajiyar hatsi mai yawa. A can garin Yusuf kuma, iyalin Yakub suna tsananin rashin abinci.
9


Mutane daga kasashe dabam-dabam suka tafi Masar domin sayan hatsi. "Dole ku tafi, ku ma," Yakub ya umarci 'ya'yansa, "ko kuma yunwa ya kashe mu." Suna isowa Masar, 'ya'yansuka shirya su saya abincin.
10


'Ya'yan Yakub suka sunkuya har kasaa gaban babbn mutum mai lura da kasar Masar. Ba su gane Yusuf dan'uwansu ba. Amma Yusuf ya san su. Yusuf ya tuna da mafarkunsa. Allah ya daga shi fiye da 'yan'uwansa.
11


Yusuf yana da wayo. Ya yi magana mai zafi sai ya yi garkuwa da dan'uwansu Simiyon. "Ku dauki abincin, ku tafi gida ku dawo da kannin ku dan'uwan ku," ya umarta. "Ta haka zan sani cewa ku ba 'yan lekan asiri ba ne."
12


'Yan'uwan suna tunani cewa watakila Allah yana hukunta su ne saboda sun sayar da Yusuf zuwa bauta shekarun baya.
13


Yakub da 'ya'yansa suke rikice. 'An mayar mana da kudinmu a cikin hatsinmu. Kuma mai mulkin ya ce dole sai mun dawo da Benjamin.' Yakub ba zai bar Bemjamin yatafi ba. Ba a dadde ba sai abincin ya kare. Dole sai 'yan'uwan sun koma Masar. Benjamin ya tafi tare da su.
14
















**Allah ya daukaka Yusuf Bawan**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Farawa 39-45**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

20

# KARSHE

8 60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**